

Amarya mai Kwaɗayi
Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 3
Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Amarya mai Kwaɗayi
Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project -American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye hakkin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN
Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright: SIL International 2009




Gata nan gata nan ku! An yi wata yarinya mai suna Asabe.
Asabe yarinya ce mai kwaɗayi.

Wata rana an ɗaura auren Asabe. An kama hanyar kai Asabe gidan miji. Asabe ta ga tukunyar nama a hanya.



Asabe tana son cin naman. Iyayen Asabe sun hana ta cin naman. Asabe ta rasa yanda za ta yi.









Bayan tafiya ta yi nisa. Sai Asabe ta ce ta manta zanenta.
Iyayenta suka ce ba damowa.
Za su saya mata wani zani.

Asabe ta sake tunani. Asabe ta ce ta manta akwatinta.
Iyayenta sun ce ta bari. Za su saya mata wani akwati.






Asabe tana son ta ci nama. Asabe ta ce ta manta ranta.
Iyayenta sun ce ta je ta ɗauko.



Asabe ta koma wurin tukunyar nama. Asabe ta buɗe ta ci nama. Naman Dodanniya ne Asabe ta ci.

Asabe ta dawo wurin iyayenta. Asabe bata iya magana. Harshen Asabe ya yi dogo. Harshenta na lilo a bakinta.



ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT

USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE

World Vision

Australian Aid

GLOBAL READING NETWORK